

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Gano Matsayinka

Yesu ya ɗauki ƙiyayyar mu domin mu sami karɓuwar Sa a wurin Uba



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Akwai wani muhimmin mataki wajen samun karɓuwa, wanda shi ne samun karɓuwar mutanen Allah. Wannan yana nufin gano matsayinka a cikin jikin Kristi.

Ka gani, a matsayin mu na Krista, ba a ware muke ba. An shigo da mu cikin dangantaka da 'yan'uwanmu Masu Bi. Wannan dangantaka na ɗaya daga cikin hanyoyin da muke samun karɓuwa a rayuwar mu ta yau da kullum. Samun karɓuwa daga wurin Uba na sama kaɗai bai isa ba. Wannan shi ne mataki na farko, kuma hakika mafi muhimmanci.

Amma, bayan wannan, dole ne a sami amincewa a cikin dangantakar mu da 'yan'uwan mu Masu Bi.

Gaba ɗaya, Krista jiki ɗaya ne, kowanne Krista kuma sashi ne na wannan jikin. Babu wanda zai iya cewa 'yan'uwa Masu Bi, "Ba na buƙatar ku." Dukan mu muna buƙatar juna. Allah ya halicci jiki ta yadda gaɓoɓin suna dogara da juna. Babu ɗaya da zai iya yin aiki yadda ya kamata shi kaɗai. Wannan ƙa'ida ta shafi kowannen mu. Ta shafe ka. Dole ne ka gano matsayinka a cikin jikin Kristi. Kana buƙatar sauran gaɓoɓin, su ma suna buƙatar ka. Gano matsayinka a cikin jikin yana tabbatar da samun karɓuwarka ta zama ɗanɗanon yau da kullum.

Idan kana kuka a cikin zuciyarka game da irin wannan haɗakar, ina ba ka shawarar ka yi wannan addu'ar: "Ya Ubangiji, ina marmarin kasancewa a gidanka, in zama sashi na iyalin ruhaniya na Masu Bi da himma. Idan akwai wasu shinge a ciki na, ina roƙonka ka kawar da su. Ka jagorance ni zuwa cikin ƙungiyar da wannan buri nawa zai cika, kuma ka taimake ni in miƙa kai gare su kamar yadda ake buƙata. A cikin sunan Yesu, amin."

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-147-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.